Lallai cewa Musa ya kasance mai kunya ne Mai yawan Suturce kansa, ba'a iya ganin komai na fatarsa saboda kunyarsa, sai suka cutar da shi daga cikin bani Isra'ila

An karvo daga Abu Huraira -Allah ya yarda da shi- ya ce manzon Allah SAW ya ce: "Lallai cewa Musa ya kasance mai kunya ne Mai yawan Suturce kansa, ba'a iya ganin komai na fatarsa saboda kunyarsa, sai suka cutar da shi daga cikin bani Isra'ila, suka ce baya vuya sai don saboda wani aibi ne daga fatarsa, kodai Albaras ko kazuwa, kuma Allah sai ya so Kuvutar da shi daga abunda suka faxa ga Musa xin, sai wata rana ya kaxaita don wanka ya sanya Tufafinsa akan Dutse, yayin da ya gama sai ya taho wajen kayansa don ya sanya, sai Dutsen ya zura da gudu da kayansa ya na cewa: Dutse kayana Dutse kayana, har sai da ya kaishi cikin Mutane sai suka ganshi tsirara a Mafi kyawun halittar Allah, kumka ya tserar da shi daga abunda suke jifansa da shi, kuma sai Dutsen ya tsaya, ya xauki kayansa sai ya sanya, sai ya fara dukan Dutsen da Sandansa, na rantse da Allah akwai tabon dukan Dutsen sau Uku ko sau huxu ko sau biyar, kuma wannan shi ne faxin sa: "Ya ku waxanda kukai Imani kada kukasance kamar waxanda suka cutar da Musa sai Allah ya kuvutar da shi daga abunda suka ce kuma ya Kasance Mai Qima a wajen Allah" (Al-ahzab: 69)

[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim suka Rawaito shi]

Annabi Musa ya kasance mai kunya ne Mai yawan Suturce kansa, ba'a iya ganin komai na fatarsa saboda kunyarsa, sai suka cutar da shi daga cikin bani Isra'ila, suka ce baya vuya sai don saboda wani aibi ne daga fatarsa, kodai Albaras ko kazuwa, kuma Allah sai ya so Kuvutar da shi daga abunda suka faxa ga Musa xin, sai wata rana ya kaxaita don wanka ya sanya Tufafinsa akan Dutse, yayin da ya gama sai ya taho wajen kayansa don ya sanya, sai Dutsen ya zura da gudu da kayansa ya na cewa: Dutse kayana Dutse kayana, har sai da ya kaishi cikin Mutane sai suka ganshi tsirara a Mafi kyawun halittar Allah, kumka ya tserar da shi daga abunda suke jifansa da shi, kuma sai Dutsen ya tsaya, ya xauki kayansa sai ya sanya, sai ya fara dukan Dutsen da Sandansa, na rantse da Allah akwai tabon dukan Dutsen sau Uku ko sau huxu ko sau biyar, kuma wannan shi ne faxin sa: "Ya ku waxanda kukai Imani kada kukasance kamar waxanda suka cutar da Musa sai Allah ya kuvutar da shi daga abunda suka ce kuma ya Kasance Mai Qima a wajen Allah" (Al-ahzab: 69) ai ku kiyayi ku kasance masu cutar da Annabi SAW kamar yadda Banu Isra'ila suka cutar da Musa, sai Allah ya tsarkake shi daga abunda suka faxa game da shi, kuma Annabi Musa ma'abocin matsayi ne a Wajen Allah